# Littafi mai Tsarki na yara
## Ke gabatar da

# Bataccen Da



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**



Yesu yana jin dadin fada wa mutane game da yafiyar Allah.  Amma shugabannin Yahudawa sun yi gunaguni game da abokantakan da Yesu yake yi da masu zunubi.  Sai Yesu ya ba da labarai guda uku domin ya nuna yadda Allah yake murna sa’ad da masu zunubi suka tuba daga zunubansu.

**Labari na farko game da wani wanda yana da tumaki dari. Daya ya bata.**

**Nan da nan sai makiyayin ya bar saura guda catsa’in da tara sai ya je ya nemi dayan da ya bata.**





**Makiyayin ya yi ta nema har sai da ya sami tunkiyan da ya bata. Sai ya dauka ya ajiye a kafadarsa ya kai shi gida cikin farin ciki. Sai ya gaya wa abokansa,**

**“Ku yi farin ciki da ni, gama na sami dan tunkiyana wanda ya bace!”**

**Yesu ya bayana cewa akwai babba farin ciki a sama a kan mutum mai zunubi guda daya wanda ya tuba.  Tuba shi ne neman gafara a kan zunuban mu – neman gafara domin a bar yin zunubi gaba ki daya!**





**Labari na biyu na Yesu game da mace ce wadda tana da kudin azurfa guda goma, watakila duka ajiyar kudin da take da shi kenan. Wani abin bakin ciki ya faru. Ta batar da daya daga ciki.**

Share!  Share!  Share!  Macen ta duba ko’ina.  A karshe sai ta samu kudin.  Ta ji dadi sosai.  Ko za ka iya fada abin da ta yi?  I’i, ta gaya wa abokanta duka!





**Yesu ya sake ce wa, “Akwai farin ciki a gaban mala’ikun Allah a kan mai zunubi guda daya wanda ya tuba.”**

**Labari na ukun wanda Yesu ya fada shi ne mafi bacin rai. Ya yi magana game da wani saurayi wanda ya bar gidan babansa.**



**A wata kasa can mai nisa, yaron ya kashe kudinsa a cikin wawanci. Yanzu mene ne zai yi? Kome ya kara lallace wa sai yunwa mai tsanani ya shigo ko'ina a garin. Yunwa zai iya kashe yaron.**



**Cikin rikicewa saboda yunwa, sai yaron ya sami aikin ciyar da aladu. Amma ba mai ciyar da shi. Har ma cin abincin aladu abin farin ciki ne a gareshi. Watakila ma ya ci. A karshe, sai tunanin yaron ya dawo masa. "Can a gida, har ma 'yan hidima suna cin abinci dakyau," yana tunani.**





**“Zan koma gida in gaya wa Babana ya yafe mini laifofina. Ban isa a kira ni dansa kuma ba. Ina ba da rai zai dauke ni a matsayin mai hidimansa.”**

**Sa'ad da yana da nesa daga gida, sai babansa ya gan shi yana zuwa. Cike da farin ciki, baban ya ruga da gudu zuwa wurin dansa mai dawowa. Sai ya sumbaci yaron, ya rungume shi.**





**“Baba, na yi laifi. Ban isa in zama danka ba.” Yaron ya so ya gaya wa babansa ya dauke shi a matsayin mai hidima. Amma baban ya katse shi. “Ku kawo riga mai kyau, takalma, da kuma zobe domin da na. Ku shirya gagarumar biki.”**

**Sai aka yi wani babban hidima saboda da wanda ya bace an sake same shi.  Yesu ya fadi labarin nan saboda ya nuna yadda Allah yana so ya karbi masu zunubi wadanda suka tuba suka dawo gareshi.**



# Bataccen Da

# Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

# a na samu a

# Luka 15

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

45

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**